## CHOCOLATE CITY DA AREWA24 NA YIN SHIRI NA MUSAMMAN KAN FITATTUN MAWAKAN AREWACIN NAJERIYA

**Agusta 23, 2016** – Chocolate City Group, mafi girman kamfanin da ke yada nishadantarwa a Afirka, tare dagidan talabijin na AREWA24, mai yada shirye-shiryensa24/7a harshen Hausa da ke Arewacin Najeriya, na sanar da gagarumar hadin gwiwar talabijin ta “Nunin Mawaka.” Nunin Mawaka, wani sabon shiri ne da zai gabatar da wani sabon yanayi na taba ka lashe da zai yi nuni akan fasihai, kuma fitattun mawaka daga Arewacin Najeriya.Kowane gajeren taba ka lashe zai bibiyi harkar wake-waken daya daga cikin mawakan Chocolate City daga kuruciya zuwa matsayin da yake a yanzu, sannan zasu yi tsokaci akan irin kwarin gwiwar da suka samu daga al’adar gidansu da kuma al’umar yankinsu. Mawakan da zasu fara fitowa a karon farko na wannan shirin hadin gwiwa tsakanin Chocolate City-AREWA24 sun hada da Ruby Gyang, Jesse Jagz, Loose Kaynon, DJ Lambo and Chopstix.

Shugaban Chocolate City Group, kuma daya daga cikin wadanda suka kirkiri kamfaninAudu Maikori, ya tofa albarkacin bakinsa akan hadin gwiwar, “muna farin ciki da alfaharin aiki da AREWA24 wajen nuna gagarumar gudunmowar da mawakan Arewacin Najeriya suke bayarwa a fagen waka a Najeriya da Afirka baki daya, kuma ba waka kadai zamu gabatarwa masu kallo a Arewacin Najeriya ba, har ma da abinda ya shafi rayuwar mawakan namu.”

Bob Reid, shugaban shirye-shirye da tsare-tsare na AREWA24 ya kara da cewa, “wannan taba ka lashe zai bawa masu kallo damar samun cikakkiyar gamsuwa akan yadda al’adun Hausa suka saka fasahar mawakan taja hankalin mutane har wadanda ba ‘Yan-Arewacin Najeriya kadai ba.Muna farin cikin tsundumawa cikin arzikin Chocolate City Group kuma mun tabbata masu kallonmu zasu sami nishadantuwa kuma su koyi sababbin darussa game da wadannan mawaka, sannan kuma su ci gaba da jin dadin wakokinsu.”

Chocolate City Group da AREWA24 sun shirya hadin gwiwar da zai fito da wani sabon shirin da zai fito da mawakan Arewacin Najeriya, kuma yayi alfahari da al’adu da fasahar Najeriya. A wani bangaren na wannan hadin gwiwa, kowane mawaki na Chocolate City zai fito a shirin nan na naku mai farin jini na AREWA24 H Hip Hop, Nomiis Gee ke gabatarwa. Chocolate City-AREWA24 Artist Showcase na farko zai zo muku ranar Juma’a, 26 August 2016, a lokacin da aka saba kallon shirin H Hip Hop da karfe 9PM; a tashar AREWA24, haka kuma taba ka lashen zai kasance a tashar AREWA24’s ta YouTube (youtube.com/AREWA24channel), da kuma dandalin sada zumunta na yanar gizo, sannan kuma da sabon App din mu da aka kaddamar, wanda za’a iya samu a Google Play da I-Tunes.

**About Chocolate City Group:** Chocolate City Group yana ajin da ake yiwa lakabi da 360-degree ya kunshi buga wakoki, shirya tarurruka, tafiyar da al’amura, da tallace-tallace da ayyukan kafafen yada labarai a Najeriya. Suna da ofisoshi a Lagos, Abuja da Nairobi, da kuma ayyukan hulda da jama’a a Ingila, Amirka, Afirka ta kudu da Ghana. Chocolate City group yana kuma kirkire-kirkire da kuma aiwatar da samar da lakabi, da kuma tafiyar da kasuwancin manyan kamfanonin da ka sani a duniya. Fasihan da suke a karkashin Chocolate City Group sune mawakan da suka fi shaharar da masana’antar waka a Afirka zata iya gabatarwa duniya. Kamar MI, Ice Prince, Vitoria Kimani, Jesse Jagz, DJ Caise da sauran su kuma su taimaka wajen mayar da wannan ya zama kamfanin wake-waken da yafi kowanne girma a Afirka.

Kano, Nigeria | The AREWA24 Channel, LLC | Lagos, Nigeria
www.arewa24.com
info@arewa24.com
+234-802-367-3730

**Game Da Arewa24:** AREWA24 (arewa24.com) gidan talabijin din Arewacin Najeriya ne na farko a tauraron Dan-Adam mai yada shirye-shiryensa 24/7 kyauta, wanda ke gabatar da shirye-shiryensa akan rayuwar Arewacin Najeriya, al'adu, matasa, kasuwanci da nishadantar da iyali. AREWA24 ta dukufa wajen habakawa da kuma cike gibin da masu magana da harshen Hausa suka rasa na shirye-shiryen Hausa a duk fadin duniya, wadanda da yawansu sukan kama tashar AREWA24 ta hanyar yanar gizo domin ganin al'adarsu da kuma ta sauran mutanen duniya. Ana dora shirye-shiryen AREWA24 na kashin kanta kowane sati a youtube.com/AREWA24channel, kuma tashar tana karuwa da masu kallonta ko da yaushe a AREWA24.com, Facebook.com/AREWA24, Instagram.com/AREWA24channel, da twitter.com/AREWA24channel. AREWA24 tana kan EUTELSAT 16A, horizontal polarization, frequency 10804, symbol rate 30000 da kuma tauraron Dan-Adam na ACTV. Abokan huldar AREWA24 sun hada da Jordan Media City, Eutelsat da Globecast. Ana rarraba shirye-shiryen AREWA24 na kashin kanta a duk fadin Arewacin Najeriya tare da hadin gwiwar hukumar talabijin ta Najeriya (NTA). Tashoshin da suka fara gudanar da wannan hadakar ta NTA-AREWA24 sun hada da NTA-Abuja, NTA-Bauchi, NTA-Kaduna, NTA-Kano, NTA-Maiduguri da NTA-Sokoto, kuma zamu ci gaba da kutsawa cikin sauran tashoshin NTA a Arewacin Najeriya gaba dayan wannan shekarar.

Kano, Nigeria The AREWA24 Channel, LLC Lagos, Nigeria
www.arewa24.com
info@arewa24.com
+234-802-367-3730